
# MY VOTE
# MY VOICE



PRESENTED BY: Monitor the future project


ZAMU YARDA KO BAZAMU YARD ABA?!
BA ZA MU YARDA!!
Sade, wata mata ce mai kauri da kuma kyau, ta tashi tsaye a gaban mutanen da take yiwa magana da karfin zuciyar ta.
AH MUN KARU A ACIKIN KUNGIYAR MU, BARKA DA ZUWA!
ZA KUYI ZABE NE KO BA ZA KUYI BA?
ZA MU YI ZABEN FA!


A INA ZAKU ISKE MU A RANAR ZABEN?
A KURIA!! A KURIA!!
A KURIA!! A KURIA!!
Monitor



ZA MA KI GAN NI A CAN KAFIN RANAR ZABEN.


MU NA BUKATAR MUTANE IRIN KA A SHEKARA TA 2023.
Ebenezer ya gyada kai da murmushi.
MUTANEN DA ZASU KYALE DUKAN ABUBUWAN DA BASA KAWO MANA DARAJA DA YAN SIYASA SUKE RABA MANA KAFIN ZABE.
NI BA NA SON KAYAN KYAUTA.


KO MUN SHIRIN ZUWAN SHEKARA TA 2023?!
MUN YI SHIRI!! MUN YI SHIRI!!
Sade ta fita da wata takarda.
DAIDAI, KOWA YA RUBUTA LAMBAR KATIN ZABEN SHI ANAN. INA SO IN TABBATAR CEWA KOWA YANA DA KATIN SHI NA ZABE.
Ebenezer ya duba Sade. Sauran yan kungiyar sun rubuta lambar su ta katin zabe. Ebenezer ya nuna alamar rudeya.
Ana nan sai Sade ta bashi takardar.
MENENE AIKIN WANNAN TAKARDAR?
TA DUBAWA YAU DA KULLUM CE.


INA DA NAWA KATIN NA ZABEN FA. AMMA BA'A GAMA SHIRYA SHI BA.
BAN GANE NUFIN KA BA.
Monitor
NA YI RAGISTA AMMA BASU BANI BA.
DAIDAINE. KAWAI KA BANI SUNAN KA DA KUMA RANAR AIHUWA ZAN KUMA DUBA MAKA ACIKIN YANAR - GIZON INEC.
YANZU?
I, BABU WUYA.


HAAA!!
KO KOMAI LAFIYA KUWA?
KATINA NA ZABE YA BACE.
BA KAI NE KA CE MIN KA KARBA BA?
Ebenezer ya duba ta. Sun zubawa junan su ido dan lokaci kadan.
KADA NA YI MAKI KARYA FA, WANCAN LAYIN NA KARBAR KATIN ZABE YAYI MANI TSAWO DA YAWA.
INA DAKIN WANKA ANAN? KAMAR IN FARA TAFIYA GIDA.
Sade ta zuba mashi ido da haushi.



Ebenezer yana zaune a kan gadon shi da kanshi acikin hanun shi. Adams, abokin shi yana tsaye akan kuma yana yin dariya.
KA SO YARINYAR NAN TUN RANAR DA KAYI MA TA MAGANA KUMA GASHI MAGANAR TA KU TA KARE A BACI?
Ebenezer yayi tsaki.
KAI MA BA KA GANE BA FA? YA AKAYI MAI DIGIRI KAMARKA BASHI DA KATIN ZABE? KO BABANA DA BAI JE MAKARANTA BA YANA DA KATIN ZABEN SHI.
SABODA KATIN ZABE NE FA.
BA KA DA HANKALI KAIMA. KANA SO IN SHIGA CIKIN DOGON LAYI A TSAKAR RANA KO?
KA YI SHURU, LAYIN AI BAI YI DOGO DA YAWA BA.
TO, SUN FADA MANA CEWA ANA RABON ALALA A HANYAR GIDAN ABINCIN GONA.
A WANCAN WURIN NA ISOLO KO?
Adam ya kada kanshi.


Ebenezer ya fita waje da sauri.


An ga Ebenezer a kan layi a tsakar rana. Layin yana tafiya a hankali. Da ya je gaba sai ya ga Sade ta na rabon abincin.


KAI?
HAAA!
KAITON KA ABINCIN YA KARE.
NA GANI CEWA KANA IYA LAYI AKAN ALALA AMMA BAKA IYA JIRAN MINTI BIYAR BA DOMIN KA KARBI KATIN ZABEN KA BA.



ME YASA BA KA FADA MANA CEWA ITA CE MAI RABON ABINCI BA?
MACE, BA KI DA ABINCI, MEYASA HAKA KENAN. KATIN ZABE, BA KI SAN MATSAYIN KI BA MA. AI WANNAN WAHALA CE.
Ebenezer ya jefa ma shi kwanon amma bai same shi ba. Ya buga ledar bredi kuma bredi ya fadi kasa.
TUNDA BA ZA KU YI ZABE BA DOMIN GWANATI TA SHIGA BA, KUN ZAMA ABIN BANZA DON HAKA KADA KU BA TA ABINCI.
KA JE KA CI WANNAN BREDIN DOMIN DAMUWAR KANKA YANZU YA FARA.
Adams ya nuna bredi.
YA FI MAKA KA JE KA KARBI KATIN ZABEN KA DOMIN KA ZABE GWANATI NAGARI.


YAYA ZAN YI KENAN?
Hannun Ebenezer ya kai kan bredin sai kuma ya fara ci.
DA FARKO KA SHIGA CIKIN ADIRESHIN YANAR-GIZOGIZON INEC SAI KA YI RAGISTA, BAYAN HAKA KA BI DOKOKINSU DAGA NAN.
BARI IN FARA CI!
KADA KA CI KA MANTA DA RAYUWAR FA. KA KARBI KATIN ZABEN KA FA.

Monitor

# Conclusion

**This discussion is not just about you, here or now. It's about what the future holds, it's about what we owe generations unborn. It's about getting your PVC today!**

@tfaafrica
@tfaafrica
thefutureafrica.com
Info@thefutureafrica.com
08022226712

